## *Wasika Mai Nuna Yawan Kauna Daga Wurin Allah Zuwa Gare Ku.*

***Yaya Na,***
Mai yiwuwa baku san ni ba, amma ni na san kome game da ku.
Zabura 139:1

Da zaman ku da tashin ku duk na sani.
Zabura 139: 2

Na saba da duk al'amuran ku.
Zabura 139: 3

Har gashin kan ku ma duk a kidaye ya ke.
Matta 10: 29-31

Na halicce ku cikin siffa ta.
Farawa 1: 27

Ta gare ni ne kuke rayuwa, kuke motsi, kuke kuma kasancewa.
Ayyukan Manzanni 17:28

Ku ma zuriya ta ce.
Ayyukan Manzanni 17: 28

Na san ku tun kafin a yi cikinku.
Irimiya 1: 4-5

Tun kuna ciki na maishe ku abin gado na.
Afisawa 1: 11-12

Ba ta hanyar kuskure na yi ku ba, kwanakin ku duka na rubuta a littafi na.
Zabura 139: 15-16

Ni na halicce ku, na kuma kayyade in da za ku zauna.
Ayyukan Manzani 17: 26

Yadda na yi ku abun banmammaki ne.
Zabura 139:14

Ni na harhada ku a cikin mahaifan ku.
Zabura 139: 13

Tun da aka haife ku, ina kiyaye ku.
Zabura 71:6

Wadanda basu san ni ba,ba za su gane maganata ba.
Yahaya 8: 41-44

Ba na nisa ko fushi, ina da cikakiyar kauna domin ku.
1 Yahaya 4: 16

Ina marmarin nuna maku ainihin kauna.
1 Yahaya 3: 1

Domin ku yaya na ne, ni kuwa Uban ku ne.
1 Yahaya 3: 1

Ina ba da kyawawan kyautai fiye da ubanni na duniya.
Matiyu 7: 11

Ni ne Uba na kwarai.
Matiyu 5: 48

Kowace kyakkyawar baiwa daga wuri na ta ke.
Yakubu 1: 17

Dukkan komai nawa ne zan kuma biya duka bukatun ku.
Matiyu 6:31-33

Shirin alheri ne na ke da shi domin ku.
Irimiya 29: 11

Ina kaunar ku da madawwamiyar kauna.
Irimiya 31:3

Yawan kyakyawan tunani da nake da shi domin ku, in da za'a kidaya shi za ya fi yashin teku yawa.
Zabura 139: 17-18

Ina murna da ku ta wurin raira waka.
Zafaniya 3: 17

Bazan fasa nuna maku alheri ba.
Irimiya 32:40

Ku zababbiyar jama'a ta che.
Fitowa 19:5

Ina marmarin dasa ku a wanan kasa da aminchi da zuchiya daya.
Irimiya 32:41

Ina so in nuna maku manyan al’amura masu girma da banmamaki.
Irimiya 33:3

Idan kun neme ni da dukan ranku, za ku same ni.
Maimaitawar Sharia 4:29

Ku nemi farin cikinku a wuri na, zan kuwa biya maku bukatunku.
Zabura 37:4

Ni ne mai aiki a zuchiyar ku.
Filibiyawa 2: 13

Ina da ikon aikatawa fiye da yadde kuke tsammani.
Afisawa 3:20

Ni ne mai ba da madawwamiyar ta’aziyya.
2 Tasalonikawa 2:16-17

Ni ne kuma Allah na dukan ta’aziyya.
2 Korantiyawa 1:3,4

Lokachin da kuna bachin zuchiya ko damuwa, ina kusa.
Zabura 34:18

Zan rungume ku yadda makiyayi ke yi.
Ishaya 40:11

Wata rana zan share maku dukkan hawaye.
Wahayin Yahaya 21:3-4

Bakin ciki, da kuka, da azaba duk zan dauke.
Wahayin Yahaya 21: 3- 4

Ni Uban ku ne kuma ina kaunar ku yadda nake kaunar da na, Yesu.
Yahaya 17:23

Ta wurin Yesu ne kauna ta take bayyanuwa.
Yahaya 17:26

Shi ne ainihin kamanni na.
Ibraniyawa 1:3

Ya zo ya nuna yana goyan bayanku. Baya gaba da ku.
Romawa 8:31

Ba na lisafta laifofin ku.
2 Korantiyawa 5:18-19

Yesu ya mutu domin ya sulhunta ku da ni.
2 Korantiyawa 5:18-19

Mutuwar sa ta zama cikakkiyar bayyanuwar kaunar sa domin ku.
1Yahaya 4:10

Na ba da komai nawa domin in  kaunace ku.
Romawa 8: 31-32

In kun karbi kyautar da na Yesu, kun kuwa karbe ni.
1 Yahaya 2:23

Ba abu da zai sake raba ku da kaunar da nake da ita domin ku.
Romawa 8:38-39

Akwai baban buki da za a yi a sama in kun zo gida.
Luka 15:7

Ni ne Uba. Ni ne Uba har'abada.
Afisawa 3:14-15

Tambayar ita ce……….za ku zama yaya na?
Yahaya 1: 12-13

Ina jiran ku.
Luka 15: 11-32

*Da yawan kauna,*
*Uban ku.*
*Allah mai Tsarki.*